# ZAKKA
# Da
# WAKAFI



**Prof. Sani Abubakar Lugga, MFR**
**The 5th Waziri of Katsina**

Rahotanni sun tabbatar da cewa talauci da rashin ayyukan yi ne a kan gaba wajen ruruta rikice-rikice da yawaita barace-barace, da sace-sace, da sauran miyagun ayyuka musamman a Jihohin Arewacin Najeriya inda Musulmi su ke tsantsa! Shekaru fiye ta arba'in, Musulmi sai addu'oi su ke ta yi wai don Allah Ya raba su da waɗannan masifu. Amma Allah tuni Ya ba Musulmi maganin waɗannan masifun ta hanyar Zakka da Awƙaf amma sun watsar da su.

Wannan Littafi ya yi bayani cewa, Hukumar Kasa ke da ikon kafa Cibiyar da zata riƙa tara Zakka daga Musulmi tana rabawa kamar yadda Allah Ya yi umurni. Misali, wajibi ne Hukumar Jihar Katsina ta kafa irin wannan Cibiya domin mutanen Jihar Katsina tsantsar su Musulmi ne. Kuma wajibi ne Hukuma ta tsare mutuncin rayuwar iyalin Musulmi, musamman Yara Kanana; kuma Hukuma ta ƙarfafa yin Awƙaf domin taimakama jama'a.

Wannan Littafin ya bayar da bayanai akan duk abinda ya shafi Zakka da Awƙaf. Sai Littafin ya ƙare da tambayar cewa, "Shin ko Musulmi ba su son kawar da talauci da barace-barace da sauran masifu da kuma tsirar da kawunan su daga azabar Allah a Lahira?"

# ZAKKA TANA TSARKAKE DUKIYA, TA GIRMA KAMAR ICCEN DA AKE BA RUWA DA TAKI; KUMA A SAMU LADAR ALLAH (SWT) WANDA YA CE AYI TA











**WAQAFI (JIMLA-AWQAF) SHI NE KAMAR GINA MASALLACI, KO MAKARANTA, KO WANI GINI MAI AMFANI, KO RIJIYA, DA SAURAN MAKAMANTAN HAKA, DOMIN AMFANIN MUTANE KYAUTA. WANNAN SADAKA CE MAI GUDANA HAR A LAHIRA**













**Na:**
**Professor Sani Abubakar Lugga, MFR**
**Wazirin Katsina Na 5**
**Professor of Management Studies**
**Doctor of Philosophy in Conflict Management**
**Fellow of the Nigerian Institute of Management**
**Fellow of the Institute of Management Consultants (Nigeria)**
**Fellow of the Institute of Professional Financial Managers (UK)**
**Fellow of the London Graduate School, London, United Kingdom**
**Key Founder and former Senior Lecturer, Al-Qalam University, Katsina**
**Visiting Prof., Ecole Superieure Universitaire, Cotonou, Benin Republic**
**Visiting Professor at St. Clements Private Swiss University, Switzerland**
**Committee Member, Nigeria Supreme Council for Islamic Affairs**
**Committee Chairman, Jama’atuNasril Islam, Kaduna, Nigeria**
**Member of Sultan Foundation for Peace and Development**
**Executive Member, Interfaith Initiative for Peace, Nigeria**
**Ambassador of Universal Peace Federation, New York**
**Member of Professors World Peace Academy, Korea**

**www.books.luggaweb.com**

**Haƙƙin Mallaka** © Prof. Sani Abubakar Lugga
© **Copyright:** Prof. Sani Abubakar Lugga

**ISBN 978-978-778-069-5**

**Ɗab’in Maɗaba’ar Lugga**
Gidan Lugga, Titin Kofar Marusa, Katsina,
Jihar Katsina, Najeriya.

**Ramadan 1446 Hijrah**
**March (Maris) 2025 Miladiyya**

**A Lura Cewa An Fara Buga Wannan Littfai A Shekarar 1438 AH (2017 AD). Yanzu An Inganta Shi**

# ABUBUWAN DA KE CIKI


| ABUBUWAN DA KE CIKI | SHAFI |
|---|---|
| GABATARWA | 7 |
| Babi Na Ɗaya<br>KAFA CIBIYAR ZAKKA A NAJERIYA | 10 |
| Babi Na Biyu<br>KAFA HUKUMAR ZAKKA A JIHAR KATSINA | 16 |
| Babi Na Ukku<br>MA'ANA DA MATSAYIN ZAKKA | 22 |
| Babi Na Huɗu<br>KASHEDI GA MARAS FITAR DA ZAKKA | 24 |
| Babi Na Biya<br>FA'IDAR ZAKKA | 26 |
| Babi Na Shidda<br>NISABIN ZAKKA | 31 |
| Babi Na Bakwai<br>ZAKKAR DABBOBI | 32 |
| Babi Na Takwas<br>ZAKKAR KUƊI | 35 |
| Babi Na Tara<br>ZAKKAR KAYAN ABINCI | 37 |
| Babi Na Goma<br>ZAKKAR KAYAN ADON MATA | 40 |
| Babi Na Goma Sha Ɗaya<br>ZAKKAR MA'ADINAI DA DUKIYAR DA<br>AKA TSINTA A KARKASHIN KASA | 42 |
| Babi Na Goma Sha Biyu<br>BAYAR DA ZAKKA | 43 |
| Babi Na Goma Sha Ukku<br>WASU BAYANAI MUHIMMAI A KAN ZAKKA | 47 |
| Babi Na Goma Sha Huɗu<br>ZAKKAR FIDDA KAI | 51 |
| Babi Na Goma Sha Biyar<br>MUHIMMANCIN WAKAFI | 53 |

# GABATARWA

## بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

**الْحَمْدُ لِلَّهِ نَحْمَدُهُ وَنَسْتَعِينُهُ وَنَسْتَغْفِرُهُ وَنَعُوذُ بِاللَّهِ مِنْ شُرُورِ أَنْفُسِنَا وَمِنْ سَيِّئَاتِ أَعْمَالِنَا**
**مَنْ يَهْدِهِ اللَّهُ فَلَا مُضِلَّ لَهُ وَمَنْ يُضْلِلْ فَلَا هَادِيَ لَهُ**
**وَأَشْهَدُ أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ وَأَنَّ مُحَمَّدًا**
**صَلَّى اللَّهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ عَبْدُهُ وَرَسُولُهُ**

*Assalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta'ala wa Barkatuhu,*

**ZAKKA** shishshike ce a cikin shikashikan Musulunci guda biyar kuma tilas ce a kan duk Musulmin da Allah Ya ba kuɗi ko dukiyar da Allah Ya wajabta Zakka a kan su. Biyan Zakka na tsarkake dukiya kuma yana zamowa sanadiyyar yalwatar arziki ga wanda ke fitar da Zakka da kuma ga ƙasa baki ɗaya. Yawan talauci a tsakanin al-Ummah a zamanin yau, ya ta'allaƙa ne ga watsi da aka yi da bayar da Zakka. Don haka ne na wallafa wannan ɗan Littafi domin faɗakar da Musulmi a kan wannan muhimmiyar ibadar Allah ta Zakka.

Na ciro wannan Littafi ne sannan na yi masa wasu ƙare-ƙare da gyare-gyare daga wani babban Littafi da na wallafa a shekarar 2016 Miladiyya mai suna, **"YI MA KAN KA HISABI, Kamin Allah Ya Yi Maka";** wanda ya ƙunshi mas'alolin rayuwa daban-daban da suka addabi Musulmi. Kuma na yi amfani da Littattafan Addinin Musulunci iri-iri da Shafukan Internet da dama da suka yi bayanai a kan Zakka da Awƙaf; musamman Shafin http://ha.islamkingdom.com

**AWKAF (watau jimlar Waƙafi),** suna nufin Sadaƙatul-Jariya, mai ma'anar "Sadaƙa Mai Gudana" kamar gina Masallatai, gina

Rijiyoyi, gina Makarantun Addinin Musulunci da na Koyon Sana'oi, bunƙasa Gonaki domin Jama'a su sami abinci kyauta, da makanamtan su.

Ina roƙon Allah Ya saka ma duk waɗanda suka taimaka wajen samuwar wannan Littafi da alheri; musamman waɗanda suka duba Babban Littafin "YI MA KAN KA HISABI" kuma suka yi gyare-gyare da bada shawarwarin inganta shi. Waɗannan bayin Allah sun haɗa da Sheikh Imam Abba Muhammad Aliyu (Babban Limamin Masallacin Juma'a a Katsina), Sheikh Imam Abubakar Ibrahim Charanchi (Shugaban Kolejin Musulunci ta Usman Fodio kuma Babban Limamin Juma'a a Katsina), Sheikh Labaran Imam Saulawa (Babban Malami a Kolejin Musulunci ta Usman Nagogo, Katsina), Prof. Muhammad Sagir Adam (Shugaban Sashen Larabci a Jami'ar Musulunci ta Katsina), Marigayi Justice Nuruddeen Abbas Mashi (Joji a Kotun Ɗaukaka Kara ta Shari'ar Musulunci ta Jihar Katsina), Dr. Abubakar Sani Lugga (Likita a Asibitin Koyarwa ta Gwamnatin Tarayya a Katsina kuma Hafizin Al-Kur'ani) da sauran bayin Allah da fili ba zai isa a zayyana dukkan sunayen su ba a nan.

Allah Ya sa duk abinda aka rubuta a wannan Littafi ya zama alheri gare mu baki ɗaya, kuma Allah Ya gafarta mana duk wani kuskure da aka yi a cikin Littafin, domin duk ɗan Adam ajizi ne. Kuma ina roƙon duk wanda ya karanta wannan Littafi da ya yi aiki da abinda ke cikin sa wanda ya yi muwafaƙa da *Kitab-was-Sunnah*, kuma ya gyara duk abinda bai yi muwafaƙa da su ba; bayan haka ya aiko ma ni ko ya aika ma Kamfanin Ɗab'in Littafin domin a gyara. Allah Shi ne Masani.

Ina godiya ga mata na, Binta da Hadiya da Azhar; da 'ya'ya na, da jikoki na, da sauran iyalan gida na da suke yi mani biyayya da kyautatawa kamar yadda Allah Ya ce a yi. Ina yi masu addu'ar

Allah ya Yi masu albarka kuma Ya saukar masu da alherin Shi, Duniya da Lahira, *Ameen.*

Ina roƙon Allah Ya jiƙan iyayen mu, Alhaji Abubakar Lugga da Hajiya A'isha, waɗanda suka rene mu kuma suka yi mana tarbiyya irin ta addinin Musulunci. Ina roƙon Allah Ya jiƙan matata Umma da ɗiyata Fatima. Ina roƙon Allah Ya sada mu da su da dukkan Musulmi a Aljannar Firdausi, *ameen.*

*Wassalamu Alaikum wa Rahmatul Lahi Ta'ala wa Barkatuhu.*

**Prof. Sani Abubakar Lugga**
**Wazirin Katsina.**

# Babi Na Farko

# KAFA CIBIYAR AYYUKAN ZAKKA DA NA AWKAF

Zakka ita ce haƙƙi mafi girma da Allah (SWT) Ya wajabta ma Musulmi a cikin dukiyar su kuma ita ce shishshike na ukku a tsarin shika-shikan Musulunci guda biyar. Allah (SWT) ya ambaci Sallah da Zakka tare a cikin Ayoyin Al-Kur'ani fiye da tamanin (80) domin girma da muhimmancin waɗannan ibadu guda biyu. Sallah na tsarkake ruhin mutane Zakka kuma tana tsarkake dukiyoyin su. Zakka ce maganin talauci da duk abubuwan da ke haddasa fitinu da masifu.

## MANYAN DALILLAN DA KE HADDASA FITINU

Musulmin Najeriya sun daɗe su na ta neman hanyoyin da za su yi maganin talauci da barace-barace da rashin ayyukan yi musamman ga matasa. Wannan kuwa ya wanzu ne sabo da tabbatarwa da aka yi cewa waɗannan mas'aloli su ke gaba wajen ruruta rikice-rikice da yawaita barace-barace, da sace-sace, da ta'addanci. Abin ban takaici kuma shi ne, duk waɗannan fitinu da masifu sun yi katutu ne a Jihohin Arewacin Najeriya inda Musulmi suke tsantsa! Ga kaɗan daga Kwamitoci muhimmai da Rahotannin su suka tabbatar da cewa talauci da rashin ayyukan yi ne a kan gaba wajen haddasa fitinu:-

1. Kwamitin Shugaban Kasa na Air Marshal Paul Dike na shekarar 2009; wanda ya binciki farkon fitinun Boko Haram a Jihohin Barno, Yobe, Kano Da Bauchi
2. Kwamitin Shugaban Kasa na Ambassador Othman Gamji Galtimari na shekarar 2011; wanda ya binciki tashe-tashen hankula a Jihohin Gabas Maso Arewacin Najeriya.

3. Kwamitin Sarakunan Jihohin Arewa na Mai Martaba Etsu Nupe, Alhaji Yahaya Abubakar, CFR, na shekarar 2011; wanda ya binciki mas'alolin rashin tsaro a Jihohin Arewa.
4. Kwamitin Shugaban Ƙasa na Sheikh Dr. Ahmed Lemu, OFR na shekarar 2011; wanda ya binciki tashe-tashen hankulan da suka faru musabbabin zaɓen Shugaban Ƙasa na 2011.
5. Kwamitin Gwamnonin Jihohin Arewa na Ambassador Zakari Ibrahim, Talban Katsina, na shekarar 2013, wanda ya binciki mas'alolin rashin tsaro a Jihohin Arewa.
6. Kwamitin Shugaban Ƙasa na Hon. Kabiru Tanimu Turaki, SAN, na shekarar 2013; wanda ya binciki kuma ya yi ƙoƙarin sasanta fitinar Boko Haram da kuma bayar da shawarwari akan mas'alolin tsaro a Najeria.

## MAGANIN TALAUCI DA RASHIN AYYUKAN YI DA FITINU DA MASIFU

Allah (SWT) Ya shar'anta Zakka domin ta yi ma Musulmi maganin talauci, rashin ayyukan yi, fitinu da masifu; amma an watsar da bayar da Zakka sai addu'oi da tarurruka ake ta yi barkatai wai don Allah Ya yi ma al-Ummar Musulmi maganin waɗannan masifu. A nan, an manta da cewa Allah (SWT) ba Ya canza ma al-Umma wani hali da ta shiga sai mutanen da ke cikin wannan al-Ummar sun canza zalayen su. Kuma an manta cewa tuni Allah Ya ba Musulmi maganin waɗannan masifun ta hanyar Zakka amma an yi biris an ƙi shan wannan maganin sai kame-kame ake ta yi! Game da canza ma al-Umma halin da ta shiga, Allah (SWT) Ya faɗi cewa,

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُغَيِّرُ مَا بِقَوْمٍ حَتَّىٰ يُغَيِّرُوا۟ مَا بِأَنفُسِهِمْ ۗ

*Lallai ne Allah ba ya canza abinda ya ke ga al-Umma sai sun canza abin da yake ga rayukkan su.* (Kur'ani 13:11).

Domin girma da muhimmancin Zakka, Allah (SWT) Ya faɗi Zakka fiye da sau tamanin (80) a cikin Al-Kur'ani Mai Tsarki. Kuma ko da yaushe, Allah Ya na haɗa Zakka da Sallah wuri guda domin nuna muhimmancin waɗannan ibadu guda biyu. Misali, Allah Ya ce,

وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱرْكَعُوا۟ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ

*Kuma ku tsayar da Sallah; kuma ku bayar da Zakka; kuma ku yi ruku'i tare da masu ruku'i* (Kur'ani 2:43).

## WA KE TABBATAR DA CEWA MUSULMI SUN FITAR KUMA SUN BAYAR DA ZAKKA?

Nauyi ne a kan Shugabannin Musulunci su kafa Ma'aikata ko Hukuma ko Cibiya (gwargwadon ikon su) wadda zata riƙa tarawa da raba Zakka kamar yadda Allah (SWT) da Manzon Allah (SAW) suka yi umurni. A zamanin Manzon Allah (SAW) da Khalifofin sa (RLA) da sauran Shugabannin Kasashen Musulunci duk an naɗa Hukumomin Zakka. Har a zamanin yau, Shugabannin Kasashen Musulunci suna naɗa Hukumomin Zakka. Domin muhimmancin naɗa masu ayyukan Zakka ne Allah Ya ce a basu daga cikin Zakka ko da mawadata ne masu yin ayyukan. Allah Ya ce,

إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلْفُقَرَآءِ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱلْعَٰمِلِينَ عَلَيْهَا وَٱلْمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمْ وَفِى ٱلرِّقَابِ وَٱلْغَٰرِمِينَ وَفِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِ ۖ فَرِيضَةً مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ

*Ita dai sadaka (Zakka) ta faƙirai ce da miskinai da* ***<u>masu aiki a kan ta,</u>*** *da waɗanda ake jan zukatansu, da bayi, da waɗanda ake bi bashi, da tafarkin Allah, da matafiya, rabo ne na dole daga Allah, Allah Masani ne Mai Hikima* (At-Tauba: 60)

A lura da cewa, idan Kasa ba Musulma ba ce zalla, to wajibi ne Shugabannin Musulmin da ke cikin irin wannan Kasa su kafa Cibiya mai zaman kanta domin aiwatar da wannan muhimmin aiki. Kuma lallai a ba Cibiyar ƙarfin da zata tara kuma ta raba Zakka kamar yadda Allah (SWT) Ya yi umurni kuma Manzon Allah (SAW) da Khalifofin Manzon Allah (RLA) suka aikata. Wannan ya zama dole ne a yi shi a haka domin bayar da Zakka dole ne kamar Yadda Allah Ya ce,

إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ

*Ita dai sadaka (Zakka) ta faƙirai ce da miskinai da masu aiki a kanta, da waɗanda ake jan zukatansu, da bayi, da waɗanda ake bi bashi, da tafarkin Allah, da matafiya,* ***<u>rabo ne na dole daga Allah</u>****, Allah Masani ne Mai Hikima* (At-Tauba: 60)

A zamanin Khalifa Sayyidina Abubakar (RLA), lokacin da wasu Musulmi suka ƙi bayar da Zakka, sai ya aika masu da cewa idan ba su bayar ba, to, zai yaƙe su domin ba zai yarda wasu Musulmi su ƙi bayar da abinda Allah Ya ce a karɓa daga gare su ba, kuma ba zai yarda wani Musulmi ya riƙa Sallah ba amma ya ƙi bayar da Zakka, domin yin haka raba abubuwan da Allah Ya haɗa wuri

ɗaya ne! Sayyidina Abubakar (RLA) ya dogara ne da inda Allah (SWT) Ya ke cewa,

خُذْ مِنْ أَمْوَٰلِهِمْ صَدَقَةً تُطَهِّرُهُمْ وَتُزَكِّيهِم بِهَا

*Karɓi sadaka (Zakka) daga dukiyoyin su domin ka tsarkake su kuma ka tabbatar da kirkin su da ita* (At-Tauba: 103)

A nan, za'a fahinci cewa tilas ne Shugabannin Musulmi su tabbatar da cewa an karɓi Zakka daga dukiyoyin Musulmi waɗanda Allah Ya aza ma Zakkar.

Kuma Sayyidina Abubakar (RLA) ya ƙara dogara da inda Manzon Allah (SAW) ya ce,

**أُمِرْتُ أَنْ أُقَاتِلَ النَّاسَ حَتَّى يَشْهَدُوا أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ وَأَنَّ مُحَمَّدًا رَسُولُ اللَّهِ، وَيُقِيمُوا الصَّلَاةَ، وَيُؤْتُوا الزَّكَاةَ؛ فَإِذَا فَعَلُوا ذَلِكَ عَصَمُوا مِنِّي دِمَاءَهُمْ وَأَمْوَالَهُمْ إِلَّا بِحَقِّ الْإِسْلَامِ**

*An umurce ni da in yaƙi mutane har sai sun shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma ni Muhammad Manzon Allah ne, kuma su* ***tsaida Sallah su bayar da Zakka.*** *Idan suka yi haka, jinin su da dukiyar su sun kuɓuta daga gare ni, sai fa ta* ***hakkoƙin Musulunci (kamar haƙƙin Zakka)****.* (Bukhari da Muslim suka ruwaito Hadisin daga Abu Huraira - RLA)

A nan za'a lura cewa Musulmi za su kuɓuta ne idan suna tsaida Sallah da bayar da Zakka; idan kuwa basu bayar da Zakka, to, tilas ne a karɓi wannan haƙƙin daga gare su. Sayyidina Abubakar (RLA) ya ce,

*Zan yaƙi duk Musulmin da ya raba Sallah da Zakka, domin Zakka haƙƙin dukiya ne da za'a karɓa tilas. Na rantse da Allah, duk waɗanda suka hana wata dabba da suke bayar wa lokacin Annabi*

*(SAW), zan yaƙe su domin hanawar da suka yi.* (Bukhari da Muslim da Nasa'i suka ruwaito Hadisin daga Abu Huraira - RLA)

## KAFA CIBIYAR AYYUKAN ZAKKA A NAJERIYA

Kasashen Musulmi, kamar Saudi Arabia, da Kuwait da sauransu, duk suna da Ma'aikatun Ayyukan Zakka da Awƙaf a Karƙashin manyan Ministoci. Wasu Kasashen kuma inda yin haka ya gagara, Musulmi suna kafa Cibiyoyin da ke yin wannan muhimmin aikin.

A nan Najeriya, wasu Jihohi sun kafa Hukumomin Ayyukan Zakka. A wasu Jihohin kuma Sarakuna Musulmi da wasu Kungiyoyin Musulunci sun kafa Cibiyoyin Zakka. Idan aka yi la'akkari da cewa Najeriya ce ta biyu a Duniya wajen yawan Musulmi, inda ake da kimamin Musulmi milyan 100 (100 million), to, lallai a yi tanadin tarawa da raba Zakka wanda ya fi na gutsuri-tsoma da ake da shi a yanzu a wasu 'Yan Jihohi da Masarautu kaɗan. Nauyin kafa Hukumar Zakka da zata yi aiki a faɗin Najeriya ya faɗa ne a kan Mai Alfarma Sarkin Musulmi da Mai Alfarma Shehun Barno da Masu Martaba Sarakunan Musulunci da Masu Girma Manyan Malaman Musulunci da Shugabannin Manyan Kungiyoyin Addinin Musulunci.

Babu wani dalilin da zai hana a kafa wannan Cibiya kuma a yi mata Rajista ƙarƙashin Dokokin Tarayya domin ta samu gindin zama a zamanance a cikin wannan Kasa. Idan aka bar wannan aiki a hannun wasu 'yan Masarautu da wasu 'yan Kungiyoyi, to, wata rana za'a wayi gari babu aikin domin waɗanda ke da zimmar tafiyar da ayyukan sun mutu kuma waɗanda suka hau gado basu da zimmar yin haka. Wannan abu ne wanda ya riga ya faru a wasu wurare kuma zai iya faruwa a wasu wuraren nan gaba, don haka ya zama wajibi a kiyaye wannan ta hanyar yin wani ingantancen tsari mai ɗorewa.

# Babi Na Biyu

## KAFA HUKUMAR AYYUKAN ZAKKA DA NA AWKAF A JIHAR KATSINA MAI MUSULMI TSANTSA

Lokacin da muke jira Allah Ya tabbatar da Cibiyar Zakka a Najeria, sai mu lura cewa Jihar Katsina Musulmi ne cikinta tsantsa domin haka wajibi ne Shugabannin Jihar su kafa Hukuma ta Musamman domin ayyukan Zakka da na Awƙaf. Hukumar zata riƙa karɓa da raba Zakka kamar yadda Shari'ah ta zayyana.

Wannan fa wani aiki ne na Shugabanni da duk sauran Musulmi wanda ya ke **wajibi, dole, tilas** a yi shi! Musulunci ba ya tabbatuwa sai Musulmi sun yarda kuma sun bi dukkan Umurnin Allah (SWT) da na Manzon Allah (SAW). Musulunci baya tabbata inda ake aiwatar da wani ɓangare (kamar Sallah) kuma a bar wani ɓangare (kamar Zakka). Allah Ya ce idan an shiga Musulunci, to, a shiga tsundum kuma gaba ɗaya.

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱدْخُلُوا۟ فِى ٱلسِّلْمِ كَآفَّةً وَلَا تَتَّبِعُوا۟ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَٰنِ ۚ إِنَّهُۥ لَكُمْ عَدُوٌّ مُّبِينٌ

*Ya ku waɗanda kuka yi imani! Ku shiga Musulunci baki ɗaya (ku bi duk dokoki da ƙa'idojin Addinin); kuma kada ku bi hanyoyin Shaiɗan, domin shi maƙiyi ne bayyananne a gare ku* (Kur'ani 2:208)

Watau babbar fa'idar kafa Cibiyar Zakka ita ce tabbatar da Addinin Musulunci a cikin zukata da ayyukan Musulmin Najeria, kuma wannan zai zamo sanadiyyar samun lafiya da zama lafiya da

gamawa lafiya ga dukkan Musulmi. **Ga wasu faidoji da ake iya samu ta kafa wannan Cibiyar Zakka:-**

1. FAIDAR TARA KUƊAƊE

Babban Bankin Najeriya (watau, *Central Bank of Nigeria*) ya bayar da ƙididdigar cewa tsakanin watan Satumba (September) na Shekarar 2016 zuwa watan Agusta (August) na wannan Shekarar 2017 Miladiyya, akwai tsabar kuɗaɗe kimanin Naira tiriliyan biyu (watau Naira milyan dubu har sau dubu biyu) a ko wane wata a hannun mutane a Najeriya (watau, *Naira currency in circulation in Nigeria*). Wannan bayani za'a same shi a shafin Intanet na Babban Bankin Najeriya, watau Central Bank:

http://www.cenbank.goɓ.ng kamar haka:-

₦ 1,794,287,000,000 - 30/9/2016

₦ 1,825,664,000,000 - 31/10/2016

₦ 1,907,863,000,000 - 30/11/2016

₦ 2,179,174,000,000 - 31/12/2016

₦ 1,994,577,000,000 - 31/1/2017

₦ 1,978,886,000,000 - 28/2/2017

₦ 1,983,633,000,000 - 31/3/2017

₦ 1,975,812,000,000 - 30/4/2017

₦ 1,897,917,000,000 - 31/5/2017

₦ 1,873,543,000,000 - 30/6/2017

₦ 1,769,085,000,000 - 31/7/2017

₦ 1,868,735,000,000 - 31/8/2017

Idan aka ƙaddara cewa a cikin 'Yan Najeriya milyan 200 rabi kaɗai ne Musulmi, watau mutane milyan 100; kuma a ƙaddara

cewa rabin waɗannan kuɗaɗen da ke hannun mutane suna hannun waɗannan Musulmi; to, wannan ya nuna cewa kimanin Naira tiriliyan ɗaya ke hannun Musulmin Najeriya kuma sun shekara guda a hannun su (Satumba 2016 zuwa Agusta 2017). Idan kuma aka ƙaddara cewa rabi ne kaɗai cikin waɗannan Musulmin kuɗaden su suka cika Nisabin Zakka, watau akwai Naira bilyan 500 ke nan da ta wajabci Zakka. A nan za'a iya yin lissafi kamar haka:-

₦ 500,000,000,000 ÷ 40 = **₦ 12,500,000,000** watau Naira bilyan goma sha biyu da rabi ke nan na Zakkar tsabar kuɗin da ke hannun Musulmi.

Forbes (www.forbes.com) a shekarar 2015 sun bayyana cewa mutumen da ya fi kowa arziki a Afirka Musulmi ne ɗan Najeriya mai kuɗi da ƙaddarori kimanin Dalar Amurka bilyan 15 da milyan ɗari bakwai (15.7 billion Dollars) watau kimanin Naira tiriliyan shidda da biliyan ɗari biyu da tamanin (6.28 trillian Naira) ke nan. Kuma a tuna cewa a waccan shekara to 2015 da wannan Musulmi shi kaɗai ya ke da Naira tiriliyan 6.28, Kasafin Kuɗin Gwamnatin Tarayyar Najeriya (Federal Goɓernment Budget 2015) jimlar sa Naira tiriliyan 4.5 ne!

Don haka idan aka yi la'akkari da irin waɗannan Musulmin da ke Najeriya, to, ba za'a yi mamakin samun Zakkar kuɗi lunkin-balunken waɗanda aka ƙiyasta a nan. A tuna cewa irin waɗannan Musulmi suna da tsabar kuɗi kuma yawancin ƙaddarorin su na kasuwanci ne domin haka sun wajabci Zakka. Sai dai kuma su kan amshi bashin manyan Bankuna da Cibiyoyin Kuɗi, amma duk wannan bai hana su bayar da Zakka ba akan abin da ya kamata.

Wannan ƙiyasi da aka yi sama yana iya yin aiki a Jihar Katsina gwargwadon arzikin mutanen Jihar. Abin kula a nan shi ne cewa

za’a iya tara milyoyin Naira a ko wace shekara a Jihar Katsina domin bayarwa ga waɗanda Allah Ya lissafa da ayyukan da Allah Ya ce a yi da kuɗaɗen.

## 2. FAIDAR TARA KAYAN ABINCI

### Shinkafa

Darektan Ayyukan Gona na Ma’aikatar Gona ta Tarayya mai kula da Jihar Kano, Alhaji Muhammad Adamu, ya yi ma ‘Yan Jarida bayanai a Kano a ranar Talata 15 ga watan Agusta 2017 lokacin da ya ke ƙaddamar da Kungiyar Masu Sussuka Shinkafa (Rice Millers’ Association of Nigeria). A cikin bayanan da ya yi, ya ce, a shekarar noma ta 2016/17 manoman shinkafa na Najeriya sun girbi ton milyan 15 (15 million tonnes) na shinkafa. Kuma a Jihar Kano kaɗai an girbi ton milyan 1.2 na shinkafar. Ya kuma ce, daga shekarar noma ta 2017/18 Najeriya zata gamsu da shinkafar da za’a noma a gida.

Wanna bayani nashi ya zo dadai da na Ministan Gona, Mr. Audu Ogbe wanda ya yi ma ‘Yan Jaridu a Abuja a ranar 5 ga watan Maris 2017, inda shi ma ya ce daga shekarar noma ta 2017/18 Najeriya zata gamsu da shinkafar da za’a noma a gida.

Duk da yake kusan duk shinkafar da ake nomawa daga Musulmin Jihohin Arewa ta ke, bari a ƙiyasta cewa kashi saba’in da biyar cikin ɗari (75%) ne kawai daga Musulmi. Wannan ya nuna cewa:-

A Najeriya baki ɗaya, ton milyan 11.25 ne na Musulmi, wanda zai bayar da Zakkar ton 1.125; wanda ke daidai da **ƙananan buhunnan shinkafa milyan 22.5**

A Jihar Kano kaɗai an samu ton milyan 1.2; wanda zai bayar da Zakkar ton 120,000 wanda ke daidai da **ƙananan buhunnan shinkafa milyan 2.4**

**Masara, Gero Da Dawa**

Hukumar Ayyukan Gona ta Amurka (United States Department of Agriculture) ta bayar da ƙiyasin kayan gona da ake nomawa a ko ina a Duniya a shafin ta na Intanet. Hukumar ta bayar da ƙiyasin noman masara, gero da dawa a Najeriya daga shekarar 1960 zuwa bara 2016. A bara Hukumar ta bayyana cewa an girbi ton milyan 7.2 na Masara, milyan 6.55 na Dawa da milyan 4.8 na Gero.

A nan ma, duk da yake kusan duk Masara, Dawa da Geron da ake nomawa daga Musulmin Jihohin Arewa su ke, bari a ƙiyasta cewa kashi saba'in da biyar cikin ɗari (75%) ne kawai daga Musulmi. Watau:-

**Masara** – ton milyan 5.4 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 54 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 5.4**

**Dawa** – ton milyan 4.9 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 49 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 4.9**

**Gero** – ton milyan 3.6 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 36 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 3.6**

## 3. FA'IDAR TARA DABBOBI

Ministan Gona na Najeriya, Mr Audu Ogbe ya yi hira da 'Yan Jaridu a Ofishin sa na Abuja a ranar 2 ga watan Yuni (June) 2016, inda ya bayyana cewa, a wani sansan (census) da aka yi a shekarar 2011 na Dabbobin da ke cikin Najeriya an gano cewa akwai Shanu milyan 19.5 da Awaki milyan 72.5 da Tumaki milyan 41.3 musamman a Jihohin Arewa.

A nan za'a ɗauka cewa duk na Musulmin Arewa ne don haka Zakkar su zata kama kamar haka:-

**Shanu** - 19,500,000 ÷ 30 = 650,000 Zakka

**Awaki** - 72,500,000 ÷ 100 = 725,000 Zakka

**Tumaki** - 41,300,000 ÷ 100 = 413,000 Zakka

**ALLAH YA YI GASKIYA!**

Idan aka bi umurnin Allah (SWT), dubi abinda a ƙalla za'a iya samu, ko ma abinda ya fi haka, ta hanyar Zakka a ko wace shekara a Najeriya:-

**Kuɗi:-** ₦ 500,000,000,000 ÷ 40 = **₦ 12,500,000,000** watau Naira bilyan goma sha biyu da rabi ke nan na Zakkar tsabar kuɗin da ke hannun Musulmi.

**Shinkafa:-** A Najeriya baki ɗaya, ton milyan 11.25 ne na Musulmi, wanda zai bayar da Zakkar ton 1.125; wanda ke daidai da **ƙananan buhunna milyan 22.5**

**Masara**:- Ton milyan 5.4 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 54 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 5.4**

**Dawa**:- Ton milyan 4.9 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 49 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 4.9**

**Gero:-** Ton milyan 3.6 ne na Musulmi; wanda zai bayar da manyan buhunna milyan 36 wanda Zakkar su na daidai da **manyan buhunna milyan 3.6**

**Shanu**:- 19,500,000 ÷ 30 = 650,000 Zakka

**Awaki**:- 72,500,000 ÷ 100 = 725,000 Zakka

**Tumaki**:- 41,300,000 ÷ 100 = 413,000 Zakka

# Babi Na Ukku

## MA'ANA DA MATSAYIN ZAKKA

Mafi girman abin da Allah (SWT) Ya wajabta ma Musulmi a cikin dukiyar su, shi ne bayar da Zakka, wadda ta zamo shishshike na ukku a tsarin shika-shikan Musulunci guda biyar. Zakka ta wajaba a kan dukkan Musulmi, ɗa, mai hankali, wanda ya mallaki abin da ya kai nisabin Zakka.

Allah (SWT) Ya wajabta bayar da Zakka fiye da wurare 80 a cikin al-Kur'ani. Ga kaɗan daga inda Allah Ya ke cewa,

وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱرْكَعُوا۟ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ

*Kuma ku tsayar da Sallah; kuma ku bayar da Zakka; kuma ku yi ruku'i tare da masu ruku'i* (Al- Baƙara: 43).

وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ۚ وَمَا تُقَدِّمُوا۟ لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ

تَجِدُوهُ عِندَ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ

*Kuma ku tsayar da Sallah, kuma ku bayar da Zakka. Kuma abin da duk kuka bayar na alheri domin rayukkan ku, za ku same shi a wurin Allah. Ba shakka Allah mai ganin duk abinda ku ke aikatawa ne* (Al-Baƙara: 110).

Bukhari da Muslim sun ruwaito Abdullahi bin Umar (RLA) yana cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce, "*An gina Musulunci a bisa abubuwa biyar, watau, shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah (SWT) kuma Annabi Muhammadu (SAW) Manzon Allah*

*ne, tsaida Salloli, bayar da Zakka, yin Azumin Watan Ramadhan da yin aikin Hajji ga wanda ke da ikon yi.*

Zakka wani kaso ne na kuɗi ko wasu kayan abinci ko wata dukiya da Allah (SWT) Ya zayyana, wadda ake fitarwa a wani lokaci bayyananne, a ba wasu mutane da Allah Ya ƙayyade a cikn Al-Kur'ani Mai Tsarki.

Zakka ita ce ibadar dukiya wadda Allah (SWT) Ya wajabta ta akan bayin Shi waɗanda ya azurta, don haka lallai a bayar da abin da Allah Ya wajabta a cikin dukiyar.

Allah (SWT) Ya fitar da mutane daga cikunnan iyayen su mata ba tare da komai ba sai jinin haihuwa da jelar cibiya. Mutane suka yi ta girma ba su da komai sai abinda iyayen su suka ba su. Sannan Allah Ya azurta su, ya ba su abin da ba su taɓa tunanin samu ba. Don haka ya wajaba a gode ma Allah, a bayar da abin da ya wajabta a kan dukiyoyi. Wannan ita ce hanyar samun kuɓuta daga azabar Allah a Duniya da Lahira, kuma hanyar da dukiya za ta tsarkaka. A nisanci hani da abin da Allah Ya wajabta a kan dukiya, domin yin haka halaka ce mai zare albarkar dukiya a Duniya kuma ta tsunduma mai ita a cikin Wuta a Lahira!

## Babi Na Huɗu

## KASHEDI GA MARAS FITAR DA ZAKKA

Allah (SWT) Ya yi kashedi mai tsanani akan duk wanda ke ƙin fitar da bayar da Zakka. Allah Ya ce,

وَلَا يَحْسَبَنَّ ٱلَّذِينَ يَبْخَلُونَ بِمَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ هُوَ خَيْرًا لَّهُم ۖ بَلْ هُوَ شَرٌّ لَّهُمْ ۖ سَيُطَوَّقُونَ مَا بَخِلُوا۟ بِهِۦ يَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ ۗ وَلِلَّهِ مِيرَٰثُ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ

*Kuma kada waɗanda suke rowa da abin da Allah Ya ba su daga falalar Shi su yi zaton haka alheri ne a gare su. A'a, yin haka sharri ne a gare su. Za'a naɗa musu abin da suka yi rowa da shi ranar al-Kiyama. Kuma gadon sammai da ƙassai duk mallakar Allah ne. kuma Allah masani ne dangane da abin da ku ke aikatawa* (Ali-Imran: 180).

...وَٱلَّذِينَ يَكْنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلْفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣٤﴾ يَوْمَ يُحْمَىٰ عَلَيْهَا فِى نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكْوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمْ وَجُنُوبُهُمْ وَظُهُورُهُمْ ۖ هَـٰذَا مَا كَنَزْتُمْ لِأَنفُسِكُمْ فَذُوقُوا۟ مَا كُنتُمْ تَكْنِزُونَ

*Kuma waɗanda su ke taskake zinari da azurfa; kuma ba su ciyar da su saboda Allah; ka yi masu bushara da azaba mai tsanani. A ranar da ake ƙona (narka) ta a cikin wutar Jahannama, a naɗe goshin su da gefensu da bayan su da ita, a ce masu, "wannan shi ne abin da kuka taskake wa kawunanku. To, ku ɗanɗani abin da ku ka kasance kuna sanyawa a taskoki (ku ɓoye)* (At-Tauba: 34-35)

Manzon Allah (SAW) ya ce, "*Duk wanda Allah ya ba shi dukiya, amma bai bayar da Zakkar ta ba, za a mayar masa da wannan dukiya ta zama maciji, wanda ba ya da gashi a kan sa saboda yawan dafin sa, a rataya ma mai hana Zakkar nan, ya na cafkar muƙamuƙin mutumin, ya na cewa, "ni ne dukiyar ka, ni ne abin da ka taskake*" (Bukhari ya ruwaito).

**MATASHIYA:** Azabar rashin fitar da Zakka ba sai a Lahira ba, a'a, Allah Ya na zare albarka da lalatar da tattalin arzikin mutane, al-ummomi da Kasashen da su ke ƙin fitar da bayar da Zakka.

## Wanda Ya Hana Zakka Saboda Bai Yarda Da Ita Ba

Duk wanda ya ce bai yarda da Zakka ba, alhali ya san wajiba ce, to ya kafirta, a ijma'in Malamai. Wannan ya zama haka ne sabo da ya ƙaryata Allah (SWT) da Manzon Allah (SAW). Kafirci kuwa dama yana nufin ka ƙaryata abin da Allah (SWT) Ya ce kuma ka ƙaryata saƙon Manzancin Annabi Muhammadu (SAW).

## Wanda Ya Hana Zakka Saboda Rowa

Wanda ya hana Zakka saboda rowa, za a tilasta shi ya bayar ko a karɓa da ƙarfi, amma ba za a kafirta shi ba, sai dai ya yi laifi babba, ya yi zunubi mai girma. Manzon Allah (SAW) ya ce, "*Babu wani ma'abocin zinari ko azurfa wanda ba ya bayar da haƙƙin su face sai ya kasance ranar Kiyama an narkar da su sun koma alluna na wuta, a gasa su a wutar Jahannama, sannan a ɗora su a kan goshin sa da bayan sa da gefen sa; duk lokacin da suka yi sanyi sai a sake gasa su a ɗora ma sa. Za a yi haka a cikin wani yini tsawon sa shekara dubu hamsin, har sai an yi hukunci tsakanin Bayi, sai ya ga hanyarsa, ko dai zuwa Aljannah, ko kuma zuwa Wuta*" (Muslim ya ruwaito). Sayyidina Abubakar (RLA) ya ce, "*Wallahi sai na yaƙi wanda ya raba tsakanin Sallah da Zakka saboda Zakka haƙƙin dukiya ce*". (Bukhari ya rawaito)

# Babi Na Biyar

# FA'IDAR ZAKKA

Bayar da Zakka tsaida ɗaya daga cikin ginshiƙan addinin Musulunci biyar ne, wadda ke kusantar da Musulmi zuwa ga Allah (SWT), kuma ya ƙara ma mutum imani da tsoron Allah.

Idan Musulmi suka fitar da Zakka, duk alherin da amfanin yin haka zai koma a kan su; idan kuma an ƙi fitarwa, to, masifar a kan su take ƙarewa tun a Duniya kamin a je Lahira a tarrar da azabar Allah!

**Ladar Allah Ga Mai Fitar Da Zakka**

Idan Musulmi ya fitar da Zakka, to, Allah zai tsarkake kuma Ya yalwata masa dukiyar sa a Duniya kuma Ya ba shi lada mai yawa wadda zai tarar a Lahira. Allah Ya kira Zakka da sunan "Sadaka" a wasu wuraren kuma da sunan "Zakka" a wasu. Allah Ya ce,

وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن رِّبٗا لِّيَرۡبُوَاْ فِيٓ أَمۡوَٰلِ ٱلنَّاسِ فَلَا يَرۡبُواْ عِندَ ٱللَّهِۖ وَمَآ ءَاتَيۡتُم مِّن زَكَوٰةٖ تُرِيدُونَ وَجۡهَ ٱللَّهِ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُضۡعِفُونَ

*Duk abin da kuka bayar na riba (kuɗin ruwa) don ya ƙaru a dukiyar mutane, to ba zai ƙaru a wurin Allah ba. Kuma abin da kuka bayar na Zakka kuna neman yardar Allah to wannan shi ne mai ninkuwa* (Ar-Ruum: 39)

يَمۡحَقُ ٱللَّهُ ٱلرِّبَوٰاْ وَيُرۡبِي ٱلصَّدَقَٰتِۗ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ كَفَّارٍ أَثِيمٍ

*Allah Ya na shafe albarkar riba (kuɗin ruwa), Ya na renon (ƙara) sadaka. Kuma Allah ba Ya son dukkan mai yawan kafirci, mai zunubi* (Al-Baƙara: 276).

A nan, Allah Ya gargaɗi ma su karɓar riba (kuɗin-ruwa) da cewa Ya na shafe albarkar irin waɗannan kuɗaɗe; kuma Ya bayyana cewa Ya na renon dukiyar da aka fitar ma Zakka ta yi ta ƙaruwa ga mai ita har illa masha'a Allah. Kuma Allah Ya bayyana masu hana Zakka da cewa su masu yawan kafirci da zunubi ne. A tuna cewa kuɗin Naira na Najeriya kimanin shekaru arba'in da suka wuce sun ɗara Dalar Amurka daraja domin 0.90 Naira ke dai-dai da Dala. Amma a yau, Naira 370 ko abinda ya yi sama da haka ke dai-dai da Dalar Amurka. To, wannan sharrin amsar kuɗin-ruwa ne!

**Zakka Na Faɗaɗa da Yaɗa Dukiya**

Zakka na faɗaɗa dukiya da yaɗa ta, saboda idan mutane da yawa suna sarrafa wani abu daga cikin dukiya, sai dukiyar ta ƙara buɗewa, ƙarin mutane da yawa su amfana da ita; saɓanin idan dukiyar ta zama tana jujjuyawa tsakanin mawadata ƙalilan kaɗai, faƙirai kasiran ba su samun komai. Misali, idan wanda ya mallaki Naira milyan ɗari huɗu (N400m) ya fitar da Zakkar kashi ɗaya cikin arba'in kamar yadda Musulunci ya zayyana, to, zai fitar da Naira milyan goma (N10m) kenan. Idan ya bayar da wannan Naira milyan goma a matsayin Zakka ga faƙirai biyu masu hankali, to, insha Allah, shekara mai zuwa za'a ga su ma sun fitar da Zakka. Idan aka ci gaba da haka, wata rana za'a wayi gari a ga cewa duk mutanen wannan al-ƙarya sun zama mawadata, wata ƙila ma a wata shekarar sai an ɗebi Zakkar wannan al-ƙarya an kai wata al-ƙaryar da suke da mabukata. Wannan yana faruwa a wasu Kasashen Musulmi kamar Kuwait, inda 'yan asalin Kasar ba'a basu Zakka.

**Zakka Ce Sanadiyyar Samun Rahamar Allah**

...وَرَحۡمَتِي وَسِعَتۡ كُلَّ شَيۡءٖۚ فَسَأَكۡتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ

*…Kuma Rahama Ta, ta yalwaci dukkan komi, zan rubuta ta ga waɗanda su ke kiyaye dokoki Na, kuma su na bayar da Zakka.* (Al-A'araf: 156).

Zakka ta na zama silar samun taimakon Allah, kamar yadda Allah Ya ce,

...وَلَيَنصُرَنَّ ٱللَّهُ مَن يَنصُرُهُۥٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَقَوِيٌّ عَزِيزٌ ﴿٤٠﴾ ٱلَّذِينَ إِن مَّكَّنَّٰهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَمَرُواْ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَنَهَوۡاْ عَنِ ٱلۡمُنكَرِۗ وَلِلَّهِ عَٰقِبَةُ ٱلۡأُمُورِ

*Allah Ya na taimakon wanda ya taimake Shi, haƙiƙa Allah mai ƙarfi ne mabuwayi. Waɗanda idan Mu ka tabbatar da su a bayan ƙasa sai su tsaida Sallah kuma su bayar da Zakka, kuma su yi umurni da yin kyawawan (ayyuka) kuma su yi hani da munanan (ayyuka). Kuma aƙibar al-amurra, ga Allah ta ke* (Al-Hajj: 40-41).

Manzon Allah (SAW) ya ce, "*Wanda ya yi sadaka da kwatankwacin dabino, daga tsarkakakken abin da ya samu (Allah ba ya karɓa abu sai mai tsarki), to, Allah Ya na karɓar wannan sadakar, Ya rene ta kamar yadda ɗayan ku ya ke renon ɗan goɗiyarsa, har wannan sadaka ta zama kamar girman dutse* ". (Bukhari da Muslim suka ruwaito).

Allah Ya na kankare zunubbai da sadakar nafila da ta farilla (Zakka), kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya ke cewa, "*Sadaka tana kankare zunubai kamar yadda ruwa ya ke kashe wuta*" (Timizi ya ruwaito).

**Zakka Na Gyara Halayen Mutane**

Zakka na gyaran halayen mutane, tana sanya mai yin ta ya zama mai karamci da kyauta da rangwame da tausayi da jin ƙai. Masu

tausayi da jinƙai kuwa, Allah Mai Rahama Ya na jin ƙan su, Ya na yi masu Rahama!

Duk mai bada dukiyar sa ko jikin sa wajen ayyukan alheri, to zai samu buɗewar zuciya, da natsuwa, kuma ya zama abin ƙauna a wurin 'yan-uwa Musulmi saboda irin amfanin da ya ke kawo ma jama'a. Zakka tana tsarkake mai yin ta daga rowa da son kai, kamar yadda Allah Ya ce,

خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ

*Ka karɓi sadaka (Zakka) daga dukiyoyinsu wadda za ka tsarkake su kuma ka tabbatar da kirkin su da ita* (At-Taubah:103)

### Zakka Na Kawar Da Gaba, Hassada Da Ganin Kyashi

A wajen zamantakewar mutane kuma, Zakka ta na bada gudummuwa mai yawa. Daga ciki akwai biya ma mabukata bukatun su, ta hanyar ba su kuɗi ko dabbobi ko hatsin abinci ko wasu dukiyoyi na Zakka.

Zakka kuma ta na kawar da gaba da hassada da ganin ƙyashi da su ke cikin zukatan faƙirai da miskinai. Domin idan faƙirai da miskinai na ganin masu dukiya suna walwala a cikin dukiyar su, kuma ba su amfanar su da ita, da kaɗan ko da yawa, to wannan zai iya jawo matsananciyar hassada da gaba tsakanin faƙirai da miskinai da kuma mawadata. Amma idan mawadata suna bada wani yanki na dukiyar su ga faƙirai da miskinai a matsayin Zakka, sai waɗannan abubuwa su gushe, a samu soyayya da haɗuwa da juna. Kuma faƙirai da miskinai su riƙa ganin girman mawadata.

### Zakka Na Karkare Talauci Daga Cikin Al-Ummah

Zakka tana karkare talauci daga cikin al-Ummah. Misali, Babban Bankin Duniya (*World Bank*) da ke ƙasar Switzerland ya bayyana

cewa, fiye da kashi 65 cikin 100 (65%) na ‘Yan Najeriya suna rayuwa a kan kuɗin da ke ƙasa da Dalar Amurka ɗaya (kimanin N370) a ko wace rana saboda tsananin talauci. Kuma Bankin ya bayyana cewa akasarin waɗannan matalauta suna a Arewacin Najeriya ne, watau inda Musulmi suke tsantsa. To, ba shakka babu wani abu ko wata hanya mafi sauri da za’a bi a kauda irin wannan matsanancin talaucin sai fitar da bayar da Zakka!

**Zakka Na Maganin Masifu**

Malamai sun yi ittifaƙin cewa yawan gobara da sauran masifu da ke faɗa ma dukiyoyi suna faruwa ne domin ƙin fitar da Zakka. Domin idan aka ƙi fitar da Zakka ta hanyar samun lada, to, ita zata fitar da kanta ta hanyar zamowa masifa! A dubi gobara iri-iri da ke ta faɗa ma manyan kasuwanni da kantunan Kasar nan. Kuma ayi zurfin tunani a kan ko masu shagunan nan da kasuwannin nan suna fitar da Zakka. A nan za’a ga cewa dalillan waɗannan masifu dai shi ne ƙin fitar da bayar da Zakka!

**Zakka Na Inganta Tsaro Da Zama Lafiya**

Duk kwamitocin bincike da rahotannin da suka bayar a kan tsaron Najeriya sun tabbatar da cewa babban abin da ke kawo rashin tsaro shi ne talauci. Zakka tana ragewa ko ma tana kauda talauci. Don haka idan aka duƙufa wajen fitar da Zakka da bayar da ita kamar yadda Allah Ya shimfiɗa, ba shakka za’a samu sauƙin ɓarayi da ‘yan fashi da masu satar mutane kai har ma da ‘yan ta’adda, waɗanda ke haddasa rashin tsaro.

# Babi Na Shidda

## NISABIN ZAKKA

Nisabi, wani kaso ne na kuɗi ko dukiyar da ake fitar ma Zakka, wanda idan kuɗin ko dukiyar suka kai shi, to, Zakka ta wajaba a cikin su.

Nisabi kuma sai ya zama mallakar mutum ne, mallaka tabbatacciya kuma cikakkiya. Zakka ba ta wajaba a cikin dukiyar da ba mallakar wani mutum ba ce, kamar dukiyar da aka tara don gina masallaci, ko dukiyar da aka yi waƙafin ta don amfanin kowa da kowa, ko dukiyar ƙungiyoyin jin ƙai da na ayyukan alheri.

Kuɗaɗe da wasu ƙaddarori sai sun shekara guda a hannun mai su sannan ake fitar masu da Zakka. "Shekara" a wajen maganar Zakka tana nufin shekarar Musulunci cikakkiya ta Hijirah. Tilas ne nisabi ya zama ya yi shekara guda a wurin wanda ya mallake shi, watau fararen wata goma sha biyu.

Amma wannan sharaɗi na kewayowar shekara guda a kan nisabi ya taƙaita ne a kan kuɗi, da kayan kasuwanci, da dabbobi. Amma kayan gona da na marmari da ma'adinai da dukiyar da aka tsinta a ƙarƙashin ƙasa ba sharaɗi ne sai shekara ta kewayo ba. A'a, su da an same su ne ake fitar da Zakkar su a nan take; kamar yadda bayanai zasu zo a cikin Babi-Babi na wannan Littafin.

# Babi Na Bakwai

# ZAKKAR DABBOBI

Dabbobin da ake fitar ma Zakka su ne, Raƙumma, Shanu, Awaki da Tumaki. Bayanin Zakkar su ya biyo faɗar Manzon Allah (SAW), "*Babu wani ma'abocin raƙuma ko shanu, ko awaki ko tumaki, wanda ba ya bayar da Zakkarsu, face sai sun zo masa ranar al-Kiyama da girma da ƙiba da tozo, suna tunkuyin sa da ƙahonin su, suna taka shi da kofatan su; duk lokacin da na ƙarshe suka ƙare sai na farko su dawo*" (Muslim ya rawaito).

### Sharuɗɗan Zakkar Dabbobi

(1) Dabbobin su shekara guda a wurin mai su, saboda faɗar Manzon Allah (SAW) cewa, "*Babu Zakka a cikin dukiya har sai ta shekara*". (Ibn Majah ya rawaito).

(2) Dabbobin su zama an tanade su ne don samun nono da 'ya'ya, amma ba waɗanda su ke aiki ba. Masu aiki su ne wanɗanda mai su ya ke amfani da su wajen noma ko ban ruwa ko ɗaukar kaya. Misali, shanu da raƙumma da ake aiki da su babu Zakka a cikin su, saboda su na cikin abin da mutum yake da buƙata na yau da kullum, watau kamar tufafin sanyawar sa ne.

(3) Idan an tanadi dabbobin ne don sayar wa, Zakkar su za ta zamo daga cikin kuɗin da ake samu, watau cikin Zakkar kayan kasuwanci idan shekara ta zagayo.

(4) Dabbobin su kai nisabin da Shari'ah ta zayyana.

### Nisabin Zakkar Raƙumma, Da Abin Da Za'a Fitar Daga Cikinsu

An karɓo daga Anas ɗan Malik (RLA), ya ce, Sayyidina Abubakar (RLA) ya rubuto masa wasiƙa ya na cewa, "*Wannan ita ce farillar da Allah (SWT) Ya wajabta wa dukkan Musulmi kuma*

*Manzon Allah (SAW) ya yi umurni da ita:- A cikin kowa ne raƙumma guda ashirin da huɗu zuwa ƙasa, cikin kowa ne guda biyar za a ba da akuya ko tunkiya guda. Idan su ka kai ashirin da biyar zuwa talatin da biyar za a ba da taguwa 'yar shekara ɗaya. Idan su ka kai talatin da shidda zuwa arba'in da biyar za a ba da taguwa 'yar shekara biyu. Idan su ka kai arba'in da shidda zuwa sittin za a ba da taguwa 'yar shekara ukku, ita ce wadda ta isa barbara. Idan su ka kai sittin da ɗaya zuwa saba'in da biyar za a ba da taguwa 'yar shekara huɗu. Wanda bai da komai sai raƙumma huɗu kawai, to babu Zakka a cikin su, sai dai in ya ga dama. Idan raƙumma suka kai biyar to za a ba da akuya ko tunkiya guda.* (Bukhari ya ruwaito).

Ga alƙalumman lissafin **Zakkar Raƙumma** kamar haka:-

| **Adadin Raƙuma** | **Abin Da Za A Bayar A Cikinsu** |
|---|---|
| 5 – 9 | Akuya ko tunkiya guda |
| 10 - 14 | Akuya biyu ko tunkiya biyu |
| 15 –19 | Akuya ukku ko tunkiya ukku |
| 20 –24 | Akuya huɗu ko tunkiya huɗu |
| 25 – 35 | Taguwa 'yar shekara ɗaya |
| 36 – 45 | Taguwa 'yar shekara biyu |
| 46 – 60 | Taguwa 'yar shekara ukku |
| 61 – 75 | Taguwa 'yar shekara huɗu |
| 76 – 90 | Taguwa biyu 'yan shekara biyu – biyu |
| 91 –120 | Taguwa biyu 'yan shekaru ukku – ukku |
| 120 zuwa sama | A cikin kowane arba'in za a ba da taguwa 'yar shekara biyu, a cikin kowane hamsin 'yar shekara ukku |

**Nisabin Zakkar Shanu, Da Abin Da Za'a Fitar Daga Cikinsu**

Mu'azu ɗan Jabal (RLA) ya ce, "*Manzon Allah (SAW) ya aike ni zuwa ƙasar Yemen, ya umarce ni in karɓa daga cikin kowane*

*shanu talatin saniya 'yar shekara ɗaya, daga cikin kowane arba'in saniya 'yar shekara biyu"* (Abu Dawud ya ruwaito).

Ga alƙalumman lissafin **Zakkar Shanu** kamar haka:-

| **Adadin Shanu** | **Abin Da Za A Fitar Daga Ciki** |
|---|---|
| 30 - 39 | Saniya 'yar shekara ɗaya |
| 40 - 59 | Saniya 'yar shekara biyu |
| 60 - 69 | Saniya guda biyu 'yan shekara ɗai-ɗai. |
| 70 – 79 | Saniya 'yar shekara ɗaya da 'yar shekara biyu. |

**Nisabin Zakkar Awaki Da Tumaki, Da Abin Da Za'a Fitar Daga Cikinsu**

An karɓo daga Anas ɗan Malik (RLA), ya ce, Sayyidina Abubakar (RLA) ya rubuto masa wasiƙa cewa, "*Zakkar tumaki da awaki waɗan da su ke kiwo idan sun kai arba'in zuwa ɗari da ashirin za a ba da akuya ko tunkiya ɗaya, idan sun ƙaru a kan haka - ɗari da ashirin zuwa ɗari biyu, za a ba da awaki ko tunkiya biyu, idan suka wuce ɗari biyu zuwa ɗari ukku, za a ba da guda ukku, idan suka ƙaru a kan ɗari ukku, to a kowanne ɗari za a ba da akuya ɗaya. Idan dabbobin da ake kiwo basu kai arba'in ba, guda ɗaya ce ta rage, to babu Zakka a ciki, sai dai in mai su ya ga dama* (Bukhari ya rawaito).

Ga alƙalumman lissafin **Zakkar Awaki Da Tumaki**

| **Adadin Tumaki/Awaki** | **Abin Da Za a Bayar** |
|---|---|
| 40 – 120 | Tunkiya ɗaya ko Akuya ɗaya |
| 121 – 200 | Tunkiya biyu ko Akuya biyu |
| 201 – 300 | Tunkiya ukku ko akuya ukku, idan sun fi haka, to a cikin kowanne ɗari za a ba da guda ɗaya. |

# Babi Na Takwas

# ZAKKAR KUƊI

Kuɗi su ne zinari da azurfa ko abin da yake a matsayin su na kuɗin takardu da wanin su, waɗanda ake amfani da su a zamanin yau.

Zakkar zinari da azurfa da abubuwan da suka jiɓince su wajibi ce, saboda Allah (SWT) Ya ce,

وَٱلَّذِينَ يَكۡنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلۡفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ

*Kuma waɗanda su ke taskake zinari da azurfa; kuma ba su ciyar da su saboda Allah; ka yi masu bushara da azaba mai tsanani.* (At-Tauba: 34)

Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce,

*Babu wani ma'abocin zinari ko azurfa wanda ba ya bayar da haƙƙin su face sai ya kasance ranar al-Kiyama an narkar da su sun koma alluna na wuta, a gasa su a wutar Jahannama, sannan a ɗora su a kan goshin sa da bayan sa da gefen sa; duk lokacin da suka yi sanyi sai a sake gasa su a ɗora ma sa. Za'a yi haka a cikin wani yini tsawon sa shekara dubu hamsin, har sai an yi hukunci tsakanin Bayi, sai ya ga hanyarsa, ko dai zuwa Aljannah, ko kuma zuwa Wuta* (Muslim ya ruwaito).

### Sharuɗɗan Zakkar Kuɗi

1. Shekara ta kewayo a kan su.
2. Cikakkiyar mallaka
3. Su kai nisabi

**Nisabin Zakkar Kuɗi**

1. Nisabin Zinari shi ne Dinari ashirin (85g gold).

Dirhami ɗaya na zinari = Giram (*gram*-g) huɗu da kwata. Don haka lissafin nisabin zinari da giram zai zama kamar haka: 4.25 × 20 = 85g na tataccen zinari.

2. Nisabin Azurfa shi ne Dirhami ɗari biyu (595g silɓer)

Dirhami ɗaya na azurfa = 2.975g. Don haka lissafin azurfa da giram zai zama kamar haka: 2.975g × 200 = 595g na tatacciyar azurfa.

3. Ana ƙaddara nisabin kuɗin takarda ne a kan ƙimar zinari ko azurfa a lokacin da za a fitar da zakkar, idan kuɗin ya kai nisabin ɗaya daga cikin su (watau zinari da azurfa) to Zakka ta wajaba.

Misali, idan da za'a ce giram ɗin zinari ɗaya yana daidai da Naira 10,000, to, Zakka ta wajaba a kan wanda ya ke da Naira 10,000 × 85 = Naira 850,000.

**Abin Da Ake Fitar Wa A Zakkar Kuɗi**

Abin da ya wajaba a fitar a Zakkar zinari da azurfa da takardun kuɗi da sauran kuɗaɗe da su ka jiɓince su shi ne rubu'in ushuri, watau kashi ɗaya cikin arba'in (2.5%). Wannan lissafi ya samo asali ne daga faɗar Manzon Allah (SAW) inda ya ce, *Idan kana da dirhami ɗari biyu, shekara ta zagayo a kan su, to za ka ba da dirhami biyar. Ba abin da za ka bayar idan kana da zinari har sai ya kai dinari ashirin. Idan kana da dinari ashirin, shekara ta zagayo a kan su, to a cikin su za ka ba da rabin dinari. Sannan abin da ya ƙaru a ci gaba da lissafi a kan haka* (Abu Dawud ya ruwaito).

# Babi Na Tara

# ZAKKAR KAYAN ABINCI

**Kwayoyi:** Su ne dukkan ƙwayar da ake aje wa, kamar gero da dawa da masara da alkama da shinkafa da makamantan su.

**’Ya’yan Itace:** Su ne duk wani ɗan icce da ake aje wa, kamar dabino da zabibi da makamantan su.

## Hukincin Zakkar Kwayoyi Da ‘Ya’yan Itace

Ba da Zakkar ƙwayoyi ko ‘ya‘yan itace wajibi ne, sabo da faɗar Allah (SWT) inda Ya ce mutane su bayar da haƙƙin sa daga ‘ya’yan itace.

وَهُوَ ٱلَّذِىٓ أَنشَأَ جَنَّٰتٍ مَّعۡرُوشَٰتٍ وَغَيۡرَ مَعۡرُوشَٰتٍ وَٱلنَّخۡلَ وَٱلزَّرۡعَ مُخۡتَلِفًا
أُكُلُهُۥ وَٱلزَّيۡتُونَ وَٱلرُّمَّانَ مُتَشَٰبِهًا وَغَيۡرَ مُتَشَٰبِهٍۚ كُلُواْ مِن ثَمَرِهِۦٓ
إِذَآ أَثۡمَرَ وَءَاتُواْ حَقَّهُۥ يَوۡمَ حَصَادِهِۦۖ وَلَا تُسۡرِفُوٓاْۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُسۡرِفِينَ

*Kuma Shi ne wanda Ya ƙaga halittar gonaki masu runfuna da akasin masu runfuna, da dabinnai da shuka mai saɓa wa ga ‘ya’yan sa na ci, da zaituni da rummani mai kama da juna da akasin mai kama da juna. (Mutane) ku ci daga ‘ya’yan itacen sa, idan ya yi ‘ya’yan,* ***kuma ku bayar da haƙƙin sa a ranar girbin sa****, kuma kada ku yi ɓarna. Lallai ne Shi (Allah) ba Ya son maɓarnata* (Al-An’am: 141).

Manzon Allah (SAW) ya yi bayanin Zakkar ƙwaya da ‘ya‘yan itace kamar haka:- *Cikin abin da sama ta shayar, wanda ya ke da jijiya, watau shukar da ta ke shan ruwa da kanta, ko dai ta hanyar jijiyoyin ta, ko kuma daga ruwan sama da na ƙoramu masu gudana, to, za a ba da kaso ɗaya bisa goma. Amma abin da aka*

*shayar (watau wanda aka shayar da ban ruwa, shi ne wanda aka sha wahala wajen fito da ruwan), to, shi za'a ba da rabin kashi ɗaya bisa goma* (Bukhari ya ruwaito)

**Sharuɗɗan Zakkar Kwayoyi Da 'Ya'yan Itace**

1. **Su zama za'a iya ajiye su**: Idan ba'a iya ajiye su, to babu Zakka a cikin su, saboda abin da ba ajiye shi ake ba to ba dukiya ba ce cikakkiya, don ba za'a iya amfanuwa da shi a gaba ba.

2. **Su zama abubuwan da ake aunawa ne**: Watau su zama ana iya auna su da ma'auni, domin ƙiyastawa, saboda faɗar Manzon Allah (SAW) cewa, "Babu Zakka a cikin ƙwaya ko dabino har sai ya kai wusiƙi biyar" (wusiƙi shi ne daidai da sa'i sittin) (Muslim ya ruwaito wannan). Saboda haka idan ba'a auna 'ya'yan itacen, kamar ganye (salad da dangin sa) ko kayan lambu, to babu Zakka a cikin irin waɗannan kayan gonar.

3. **Su zama mutum ne ya shuka su a gonar sa**: Idan shukar ta fito da kanta ne, kamar itacen cikin daji, to babu Zakka a kan su.

4. **Su kai nisabi**: Nisabin kwayoyi da 'ya'yan itace shi ne wusiƙi biyar, kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya bayyana. Don haka nisabin sai ya zama sa'i ɗari ukku, wanda ya yi daidai da 612 kg na kyakkyawar alkama.

**Matashiya:-** Ana iya haɗa kala-kala na 'ya'yan itacen, idan dai iri ɗaya ne, don a samar da nisabi, amma ba'a haɗa wani dangi daban da wani don samar da nisabi, kamar a haɗa gero da dabino.

**Lokacin Bada Zakkar Kwayoyi Da 'Ya'yan Itace.**

Ba a sharɗanta cewa sai shekara ta kewayo ba a kan Zakkar kayan gona da 'ya'yan itace, Allah Ya ce,

وَءَاتُوا۟ حَقَّهُۥ يَوْمَ حَصَادِهِۦ

*Ku ba da haƙƙin sa a ranar girbin sa* (Al-An'am: 141)

Kuma Zakkar ƙwayar kayan gona tana wajaba daga lokacin da ƙwayar ta yi ƙwari. 'Ya'yan itace kuma idan sun fara nuna, yadda za'a iya ci.

Wanda duk ya sayar da ƙwayar kayan gona bayan Zakka ta wajaba a kan su, to wannan Zakkar tana kan mai sayarwa, amma ba a kan mai saye ba saboda mai sayarwa ne ya mallaki abin lokacin da Zakkar da wajaba a cikin su.

**Zakkar Da Ta Wajaba A Kan Kwayoyi Da 'Ya'yan Itace.**

1. Kashi ɗaya bisa goma (10%) yana wajaba a cikin abin da aka shayar da shi ba da wata wahala ba, kamar wanda ruwan sama, ko ruwan ƙoramu masu gudana suka shayar.
2. Rabin kashi ɗaya bisa goma (5%) yana wajaba cikin abin da aka shayar da wahala, kamar wanda aka shayar da ruwan rijiyan da aka jawo da hannu.
3. Kashi ukku cikin kashi huɗu na ɗaya bisa goma (7.5%) yana wajaba a cikin abin da aka shayar da shi da duka hanyoyin biyu da aka ambata a sama, watau kamar wanda aka fara shayar da shi da ruwan sama a tsawon wani lokaci, wani lokaci kuma aka ida shayarwa da ruwan rijiya.

**Lalacewar Kwayoyi Ko 'Ya'yan Itace**

Idan ƙwayoyin kayan noma ko 'ya'yan itace suka lalace ba tare da sakacin mai kayan ba, to babu Zakka a kan su. Idan kuma wanda ya mallake su ne ya lalata su da kan sa bayan Zakka ta wajaba a kan su, to Zakkar tana nan a kan mai kayan, wajibi ne ya bayar da ita, komin tsawon lokaci. Watau yana iya bayar da wasun su ko kuma ƙimar su.

# Babi Na Goma

# ZAKKAR KAYAN ADON MATA

Kayan adon mata kala biyu ne, watau kayan adon zinari da na azurfa, da kayan adon da ba na zinari da azurfa ba ne.

## 1. Kayan Adon Zinari Da Azurfa

**Kashi na farko**: Kayan adon zinari da azurfa waɗanda aka tanada don ajiye wa da taskakewa, ko kuma don a yi kasuwanci da su, to, Zakka wajibi ce a kan waɗannan.

**Kashi na biyu**: Kayan adon zinari da azurfan da aka tanada don yin amfani da su wajen kwalliya, to nan akwai fahimta biyu daga Malamai kamar haka:-

(i) Wasu Malami sun ce ba ya wajaba a bayar da Zakka a cikin kayan adon mata waɗanda su ke amfani da su ko da na zinari da azurfa ne. Hujjar su ita ce, saboda ba dukiya ba ce wadda ta ke ƙaruwa, kurum wani abu ne na mutum da a ke amfani da shi kamar riga da wando da abaya da alkyabba da sauran kayan sutura; kuma kayan buƙatar mata ne da adon sun a yau da kullum. Ita kuwa Zakka tana wajaba a ƙa'ida cikin dukiyar da ke haɓaka, kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya bayyana.

(ii) Wasu Malaman kuma su ka ce, abin da ya fi shi ne a fitar ma waɗannan kayan da Zakka, tun da dai na zinari da azurfa ne, domin a kuɓutar da kai. Waɗannan Malaman sun bayyana cewa, wata rana wata mata ta zo wajen Annabi (SAW) tare da 'yar ta wadda ke sanye da manya-manyan warwaro na zinari a hannuwan ta, sai Manzon Allah (SAW) ya ce ma matar, *"Ko kina ba da Zakkar waɗannan warwaron?"* Sai matar ta ce, *"A'a".* Sai ya ce ma ta , *"Yanzu za ki so Allah Ya yi ma ki warwaron wuta da su ranar al-Kiyama?"*(Abu Dawud ya ruwaito). Kuma Malaman

suka ci gaba da cewa, abin da ya fi shi ne a yi taka-tsantsan da irin wannan mas'ala kuma a fitar da Zakkar kayan adon mata na zinari da azurfa waɗanda aka tanade su don amfani da kwalliya, don wannan magana, ta fi kuɓutar da kai. A nan, irin waɗannan Malaman sun tunatar da cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce, "*Ka bar abin da ya ke sa ka kokwanto, ka tafi zuwa ga abin da ba ya sa ka kokwanto*"(Bukhari ya ruwaito).

**2. Kayan Adon Da Ba Na Zinari Da Azurfa Ba**

Kayan adon mata waɗanda ba na zinari da azurfa ba, (duk da yake wasunsu ma sun fi zinari da azurfa daraja da tsadar kuɗi) kamar na daimon (diamond), yaƙutu, lu'ulu'u da makamantan su, waɗannan babu Zakka a cikin su, duk irin yawan da su ka yi. Sai dai in an tanade su ne don kasuwanci, to, sai su shiga cikin kayan kasuwancin da ake fitar ma Zakka.

# Babi Na Goma Sha Ɗaya

# ZAKKAR MA'ADINAI DA DUKIYAR DA AKA TSINTA A KARƘASHIN ƘASA

**Ma'adinai** su ne duk abin da ake fitar wa daga ƙasa, wanda ba jinsin ƙasar ba ne, kamar zinari, azurfa, ƙarfe, jauhari, dalma da wanin su.

**Dukiyar Da Aka Tsinta A Karƙashin Kasa** ita ce dukiyar da aka samu an bizne ta a ƙarƙashin ƙasa amma ba'a san mai ita ba, kamar sarrafaffen zinari ko azurfa.

Wajibi ne a bayar da Zakkar ma'adinai da dukiyar da aka tsinta a ƙasa, saboda faɗar Allah (SWT),

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنفِقُواْ مِن طَيِّبَـٰتِ مَا كَسَبۡتُمۡ وَمِمَّآ أَخۡرَجۡنَا لَكُم مِّنَ ٱلۡأَرۡضِۖ

*Ya ku waɗanda suka yi imani, ku ciyar daga daɗaɗan abubuwan da ku ka sana'anta da kuma abin da Mu ka fitar ma ku daga cikin ƙasa* (Al-Baƙarah : 267)

Manzon Allah (SAW) ya bayyana cewa,

*A cikin dukiyar da aka tsinta a ƙasa za'a ba da kashi ɗaya bisa biyar (a matsayin Zakka)* (riwayar Bukhari da Muslim).

**Sharuɗɗan Zakkar Dukiyar Da Aka Tsinta A Karƙashin Kasa**

Babu wasu sharuɗɗa wajen fitar da Zakkar dukiyar da aka tsinta a ƙasa, watau nan take da mutum ya tsinta sai ya fitar da Zakkar ta kai tsaye.

# Babi Na Goma Sha Biyu

# BAYAR DA ZAKKA

## WAƊANDA A KE BA SU ZAKKA

Masu cin Zakka su ne waɗan da suka cancance ta, su ne rukunnai guda takwas da Allah Ya iyakance su a cikin Al-Kur'ani Mai Tsarki,

إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي
ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ
عَلِيمٌ حَكِيمٞ

*Ita dai Sadaka (Zakka) ta faƙirai ce da miskinai da masu aiki a kanta, da waɗanda ake jan zukatansu, da bayi, da waɗanda ake bi bashi, da tafarkin Allah, da matafiya, rabo ne na dole daga Allah, Allah Masani ne mai Hikima* (At-Tauba: 60)

1. **Faƙirai:** Faƙirai su ne waɗanda basu da isashshen abin da zai biya masu buƙatarsu, da buƙatar iyalansu, ta abinci abin sha, tufafi da wurin zama.

2. **Miskinai:** Miskinai su ne waɗanda basu mallaki ko abincin yini guda ba, kamar naƙasassun da ba su iya neman komi, ko maras lafiya da ya ke kwance, ko waɗanda bala'i ya faɗa masu kamar na ta'addanci da makamantan waɗannan.

3. **Masu Aiki A Kan Ta:** Masu Aiki A Kan Ta su ne waɗanda suke tattara Zakka, waɗanda Shugaban Musulmi ya naɗa, kuma su ke raba Zakkar ga waɗanda Allah Ya ce a ba su. Waɗanda su ke aikin tattara Zakka za'a basu Zakka ko da masu wadata ne.

4. **Waɗanda Ake Jan Zukatansu Zuwa Musulunci:** Su ne waɗanda ba Musulmi ba, kuma a ke sa ran Musuluntar su idan an ba su Zakka, ko kuma a samu kamewar su daga yi ma Musulmi sharri, ko kuma a ƙara masu ƙarfin imani don su Musulunta, ko su kare wa Musulmi wasu maƙiyan su. Waɗannan za'a basu abin da zai jawo zukatan su daidai gwargwado daga Zakka.

5. **Bayi:** A nan ana nufin Bayi waɗanda aka rubuta masu fansa saboda kowane daga cikin su ya zama ɗa, mai ikon tasarrufi, ya zama mutum mai amfani a cikin al'ummarsa, ya kuma samu damar bautawa Allah kamar yadda ya dace. Waɗanda aka kama Musulmi a wajen yaƙi suma suna shiga ƙarƙashin Bayi, za a iya fansar su da kuɗin Zakka

6. **Waɗanda Ake Bi Bashi:** Waɗanda ake bi bashi, kashi biyu ne, **Na farko:** Wanda ake bi bashi sabo da wata buƙatar sa ta kan sa da ya yi, sai a ba shi abin da zai biya bashin daga Zakka muddin dai bai da hali ko hanyar biyan bashin. **Na biyu:** Wanda ake bi bashi saboda wani sulhu da ya yi tsakanin Musulmi, sai a ba shi abin da zai biya bashin daga Zakka, ko da mai wadata ne.

7. **Saboda Allah (Fisabilillahi):** Su ne waɗanda suke ayyukan Jihadi saboda Allah. Za'a ba su abin da zai ishe su don yin jihadin. Sauran ayyukan da'awa waɗanda su ke cikin Jihadi za su shiga cikin wannan ɓangare, idan ba su samu abin da za su yi aikin da shi ba daga sadaka. Hakanan za'a ba wanda ya ke da ƙarfi, mai iya nema, idan ya zama ya shagalta wajen neman ilmin Addini, kuma bai da kuɗi, saboda neman ilmi Jihadi ne a kan tafarkin Allah. Amma idan wanda zai iya nema ya bar aiki ya shagalta da nafiloli, to, ba za'a ba shi Zakka ba, sabo da amfanin ibada ya tsaya a kan mai yin ta, saɓanin ilmi wanda zai yaɗu ga jama'a.

8. **Matafiyi:** Shi ne matafiyin da guzuri ya yanke masa a tafiya, watau ba shi da sauran kuɗin da za su ishe shi ya kai inda za ya ko ya koma gida. Za'a ba shi abin da zai kai shi garin su daga Zakka, ko da kuwa mawadaci ne a garin su.

**Faɗakarwa**

1. Ba sharaɗi ba ne sai an ba dukkan waɗannan takwas ɗin da aka ambata a yayin raba Zakka, a'a ya wadatar idan aka ba wani ɗaya daga cikin takwas ɗin.

2. Waɗanda ba su cikin Rukunnai Takwas, ba'a ba su Zakka, ko da kuwa ayyukan alheri ne, kamar gina masallaci, makaranta, asibitoci, da sauran ayyukan alheri makamantan waɗannan. Irin waɗannan ayyukan sai dai a yi su da sadaka.

**WAƊANDA BA'A BA SU ZAKKA**

1. **Mawadata Da Masu Aiki Karfafa:** Wannan ya biyo bayan faɗar Manzon Allah (SAW*), "Babu rabon mawadaci ko mai aiki mai ƙarfi a cikin ta (Zakka)"* (Abu Dawud ya ruwaito).

2. **Iyaye, 'Ya'ya, Matan Aure, Da Waɗanda Ciyarwar su Ta Wajaba A Kan Mai Bayar da Zakkar:** Ba ya halatta mutum ya bayar da Zakka ga wanda ya wajaba mutumin ya ciyar da su, kamar iyaye, da kakanni, da 'ya'ya, da jikoki; sabo da ciyarwar da ta wajaba a kan sa ta wadatar da su daga basu Zakka.

3. **Kafiran Da Ba Waɗanda Ake Jan Zukatan Su Ba Ne Zuwa Musulunci:** Ba ya halatta a ba kafiri Zakka matuƙar dai ba jan zuciyar sa za'a yi zuwa Musulunci ba, ko ya kare Musulmi daga abokan gabar su ba, ko kada ya yi ma Musulmi wani sharri.

4. **Iyalan Gidan Annabi (SAW):** Zakka ba ta halatta ga Iyalan Gidan Annabi (SAW) don girmama su da basu daraja, kuma ba ta halatta ga Bayin gidan sa, saboda faɗar Annabi (SAW),

*Sadaka ba ta halatta gare mu, kuma bararrun Bayin mutane suna cikin su"* (Tirmizi ya ruwaito)

5. **Bawan Da Aka Mallaka:** Ba'a ba da Zakka ga Bawan da wani ya mallaka, saboda dukiyar Bawa ta mai gidan sa ce, idan aka ba shi Zakka sai ta zama mallakin mai gidan sa, saboda ciyarwar sa tana kan mai gidan sa. Amma Bawan da aka rubuta masa fansa baya cikin wannan hukuncin, shi za'a iya ba shi Zakkar da zai biya fansar da aka rubuta masa.

# Babi Na Goma Sha Ukku

# WASU BAYANAI MUHIMMAI A KAN ZAKKA

### Lokacin Fitar Da Zakka

Wajibi ne a fitar da Zakka da zarar lokacin ta ya yi, indai akwai iko. Ba ya halatta a jinkirta ta sai da lalura, kamar ya zama dukiyar tana wani gari mai nisa daga inda mai ita ya ke, ko kuma ya zamana mai dukiyar an tsare shi, ko makamancin haka.

### Wurin Da Ake Fitar Da Zakka

An fi so a fitar da zakka a cikin mutanen da dukiyar ta ke cikin su, sai dai ya halatta a ɗauki Zakka daga wani gari zuwa wani gari na kusa ko na nesa don wata buƙata. Misali, kamar a ce garin da ke nesa ɗin ya fi talauci, ko kuma mai fitar da Zakkar ya zama yana da 'yan-uwa matalauta a wancan garin mai nisa, saboda a cikin ba 'yan-uwan sa Zakka akwai maslaha da sada zumunci.

### Wanda Ya Fi Cancanta A Ba Shi Zakka

Ya kamata wanda zai fitar da Zakka ko Hukumar da zata raba Zakka su yi ƙoƙarin neman wanda ya fi dacewa a ba shi, watau wanda ya fi buƙata. Lokacin da abubuwan da su ke sa a ba mutum Zakka su ka yi yawa a kan wani mutum, to shi ya fi cancanta fiye da wanda ba shi ba.

### Bayar da Kima A Zakka

Asali dai shi ne fitar da Zakka daga cikin abin da aka wajabta, sai dai saboda wata buƙata ko maslaha ko lalura; ya halatta a ba da ƙimar Zakkar. Misali, za'a fitar da Zakka daga dukiyar da aka riga aka sayar wadda ta isa Zakka amma ba'a fitar da Zakkar ba har

aka sayar. To, a nan, sai a ƙimanta abinda ya kamata a fitar a bayar da dukiya makamanciyar wadda aka riga aka sayar.

### Zakkar Kayan Gonar Da Aka Yi Hayar Gonar

Zakkar kayan gona na kan mai haya, ba a kan mai gona ba.

### Hukumar Kasa A Kan Zakka Da Haraji

1. Zakkar kuɗi Hukuma ce zata tara kuma idan an ajiye kamin a raba, Hukumar ce za ta kula da ita. Watau ba za'a bar masu bayar da Zakkar su yi yadda suka ga dama da ita ba. Idan Hukuma ta yi rauni wajen ɗaukan wannan nauyi, to sai ya zama a kan wuyan dukkan Musulmi, watau su san yadda za su tabbatar da adalci a kan wannan mas'ala, misali su na iya naɗa amintattu su tafiyar da al-amarin.
2. Haraji ba ya zama a madadin Zakka, saboda Zakka ibada ce daga cikin ibadojin Musulunci, amma Haraji wani abu ne na zamani, don haka Haraji ba ya wadatarwa ga barin Zakka. Sai dai yana da kyau idan Hukuma ta sanya Haraji, to, sai mutum ya biya domin zaman lafiyar sa da ci gaban Kasa.

### Zakkar Mutumen Da A Ke Bin Shi Bashi

Idan ana bin mutum bashin da ya cinye dukiyar sa ko kuɗin sa duka, to, Zakka ba ta wajaba a kan shi ba. Amma idan bashin bai cinye dukiyar ko kuɗin ba duka, to, sai ya cire abin da ake bin sa bashi, ya fidda Zakkar abin da ya rage na dukiyar ko kuɗin idan abin da ya ragen ya kai nisabi. Misali, idan Mutum yana da Naira dubu ɗari (N100,000), kuma nisabin wannan shekarar Naira dubu ɗari ne, to, babu Zakka a kan sa, saboda bashin ya cinye nisabin Zakkar. Amma idan bashin da ake bin sa Naira dubu arba'in ne (N40,000), kuma yana da Naira dubu ɗari da hamsin (N150,000) to zai cire abin da bashin zai ci, watau Naira dubu arba'in, zai

zama saura Naira dubu ɗari da goma (N110,000), wadda zai fitar ma Zakka.

**Zakkar Bashin Da Mutum Ya Ke Bi**

Idan mutum na bin wani bashi, kuma da alamar zai yi wahala a biya shi bashin, kamar a ce wanda ya ke bi bashin ya talauce, ko kuma ya yi musun bashin, to Zakka ba ta wajaba akan wannan kuɗin. Amma idan mai kuɗin ya karɓi kuɗin daga baya to sai ya fitar da Zakkar shekara guda.

Idan kuma ba za'a ƙi biyan sa bashin ba, kamar ya zama wanda ake bi bashin ba mai jinkirin biyan bashi ba ne, kuma yana da niyyar biya, to wajibi ne a kan wanda ya ke bin bashin ya fitar da Zakkar bashin a duk shekara, saboda kamar kuɗin yana wajen shi ne.

**Zakkar Dukiyar Haramun**

Dukiyar haramun ita ce, dukkan dukiyar da Shari'ah ta hana a mallaka, ko a yi amfani da ita, kamar kuɗin da aka samu daga kasuwancin giya, ko kuɗin ruwa (riba), ko kuɗin da aka sato, ko kuɗin da aka saida alade, da makamantan su. To, irin wanna dukiya wadda ta ke haramun ce a karan-kanta, ba wadda ake wa Zakka ba ce, sabo da ba'a mallake ta ba cikakkiyar mallaka, wadda sharaɗi ne na wajibcin Zakka. **Ga yadda ya kamata a yi da Dukiyar Haramun:-**

(1) Wanda ya ke da dukiyar haramun da ya samu ta hanyar da ba ta dace ba, to wannan dukiyar ba mallakin sa ba ce, komin daɗewa da aka yi. Wajibi ne ya mayar da ita zuwa ga mai ita, ko wanda ya mallake ta, ko magajin ta in ya san shi, idan kuwa ya ɗebe ƙaunar gano shi, to wajibi ne ya ciyar da ita ta hanyar alheri don ya kuɓuta daga gare ta, kuma ya yi nufin sadaka ga mai ita. Sannan ya bi wannan da kyakkyawar tuba ga Allah.

(2) Idan mutum ya karɓi ladan aikin haramun da ya yi, to ya sarrafa kuɗin ta ayyukan alheri, kada ya mayar wa wanda ya ba shi, saboda idan ya mayar masa, ya taimaka a kan aikin saɓo. Sannan ya bi wannan da kyakkyawar tuba ga Allah.

(3) Ba a mayar da dukiyar haramun zuwa ga wanda ya bayar da ita, in dai yana nan kan mu'amalar sa ta haramun, kamar kuɗaɗen ruwa (riba) daga Bankuna. Za'a sarrafa su ne a ayyukan alheri. Sannan a bi wannan da kyakkyawar tuba ga Allah.

(4) Idan mayar da haƙiƙanin dukiyar haramun ya yi wuya, to sai a mayar da kwatankwacin ta, ko ƙimar ta ga mai ita, in an san shi, in kuwa ba'a san shi ba sai a sarrafa kwatankwacin ta ko ƙimar ta a ayyukan alheri, da niyyar sadaka ga mai ita.

Domin samun cikakken bayani a kan waɗannan mas'aloli guda 4 da aka zayyana a sama sai a duba littafin "*Kadaya Fiƙihiyya Mu'asira*" na Dr. Salahus Sawi, shafi na 61 zuwa gaba.

# Babi Na Goma Sha Huɗu

# ZAKKAR FIDDA KAI

**Zakkar Fidda Kai** sadaka ce wadda Manzon Allah (SAW) ya wajabta ta. An kira ta Zakkar Fidda Kai ne domin tana wajaba idan an gama Azumin Watan Ramadan gaba ɗaya.

## Hukuncin Zakkar Fidda Kai

Zakkar Fidda Kai wajibi ce akan dukkan Musulmi wanda ya mallaki sa'i ɗaya na abinci fiye da yawan abin da zai ciyar da iyalansa. Mai ba da Zakkar zai fitar ma kan sa da duk wanda ciyar da shi ta ke kan sa, har da ɗan jariri.

Dalilin wannan Zakka shi ne abin da aka ruwaito daga Ibn Umar (RLA) wanda ya ce,

*Manzon Allah (SAW) ya wajabta Zakkar Fidda Kai, sa'i ɗaya na dabino, ko sa'i ɗaya na sha'ir. An wajabta ta a kan bawa, da ɗa, namiji da mace, babba da yaro daga cikin Musulmi. Manzon Allah (SAW) ya yi umurni a bayar da ita Zakkar kafin mutane su fita Sallar Idi* (Bukhari da Muslim suka ruwaito).

## Lokacin Da Ake Fitar Da Zakkar Fidda Kai

An fi son a fitar da Zakkar a ranar Idi, bayan alfijir ya ɓullo kafin Sallar Idi. Kuma ya halatta a gabatar da ita kafin ranar idi da kwana ɗaya ko biyu, saboda Sahabbai (RLA) sun yi haka. Ba ya halatta a jinkirta ta har bayan Sallar Idi, sabo da hadisin Ibn Umar wanda ya gabata in da yake cewa *"Manzon Allah (SAW) ya yi umurnin a ba da ita kafin fitar mutane zuwa Sallar Idi".*

Haka ma a cikin hadisin Abdullahi Ibn Abbas (RLA), Manzon Allah (SAW) ya ce, *"Wanda ya bayar da ita kafin Sallar Idi, to*

*Zakka ce karɓaɓɓiya, wanda kuwa ya bayar da ita bayan Sallar, to sadaka ce daga cikin sadakoki"* (Abu Dawud ya ruwaito).

### Abin Da Ake Fitarwa A Zakkar Fidda Kai

Kowane mutum sa'i ɗaya ne a ke fitar ma shi, daga cikin abincin da yawancin mutanen wurin su ke ci, kamar gero, dawa, masara, shinkafa, dabino, alkama, da makamantan su. Sa'i ɗaya na kyakkyawar Alkama ya na daidai da kilo biyu da giram arba'in (2.4 kg).

### Waɗanda Ake Ba Zakkar Fidda Kai

Ana bayar da Zakkar Fidda Kai ga waɗannan mutanen kashi takwas waɗanda Allah (SWT) Ya ce a ba su Zakka, watau:-

إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ

*Ita dai Sadaka (Zakka) ta faƙirai ce da miskinai da masu aiki a kanta, da waɗanda ake jan zukatansu, da bayi, da waɗanda ake bi bashi, da tafarkin Allah, da matafiya* (At-Tauba: 60)

# Babi Na Goma Sha Biyar

# MUHIMMANCIN WAƘAFI (AWƘAF)

Musulunci ya yi tanade-tande domin kawar da talauci da wahaloli tsakanin mutane, musamman tsakanin masu dukiya da matalauta. Bayan Musulumci ya tabbatar da tilastawa a bayar da Zakka domin masu dukiya su taimaka ma matalauta, sai kuma Musulunci ya kawo taimakawa ta Sunnah wajen Waƙaf (Waƙafi da harshen Hausa), mai jimla da Awƙaf. Wakaf dai a taƙaice shi ne, **"Sadaukar Da Dukiya Domin Allah A Musulunci"**

An samo Al-Waƙfu da harshen Larabci daga kalmar "waƙafa", jami'insa kuwa shine "Awƙaf". Wannan yana ma'ana da cewa "ya tsaida abu, kuma ya kiyaye shi, kuma ya bayar da shi har abada".

## ASALIN YADDA AKA SHAR'ANTA WAKAFI:

Waƙafi Sunnah ce tabbataciya daga Manzon Allah (SAW), lokacin da Sayyidina Umar (RLA) ya ce:

*"Ya Manzon Allah! Lallai na samu dukiyar gona da lambu a Khaibar irin wadda ban taba samun irin ta ba a rayuwa ta, meye za ka umurce ni da in yi da ita? Sai Ma'aikin Allah (SAW) yace: "In ka so ka tsare asalin ta, kayi sadaka da ita ba tare da an sayar da asalin ta ba, kuma ba za'a kyautar ba, kuma ba za'a gada ba."* (Bukhari, Muslim, Tirmizi, Nasa'i, Abu Dawud, Ibn Majah da Ahmad ne suka ruwaito).

Sai Umar (RLA) ya sadaukar da ita ga talakawa da 'yan uwa na kusa da bayi da kuma saboda ɗaukaka Addinin Musulunci da matafiya da kuma baƙi. Kuma babu laifi ga wanda yake kula da ita da ya ci daga ciki ba tare da yin barna ba. Misalan Waƙafi sun haɗa da, Masallatai, Rijoyoin Ruwa, Makarantun Addinin

Musulunci, Makarantn Koyon Sana’a, da dai abubuwa irin waɗannan.

Anan ya kamat a fahimci cewa, akwai dukiya tabbatacciya wadda za’a iya kimanta ta amma ba’a iya ɗaukarta, kamar filin gona ko gida. Ko kuma dukiya wadda za’a iya ɗauka kamar; littattafai da tufafi, dabbobi da kuma kayan yaƙi.

## HIKIMAR SHAR’ANTA WAKAFI

An kwaɗaitar da duk wanɗanda Allah ya yalwata masu dukiya da su ƙara biyayya ga Allah ta hanyar yawaita yin ɗa’a gare Shi, kuma su yawaita neman kusanci ga Allah ta hanyar ware wani abu na dukiya tsayayya, abin da asalin ta zai dawwama, kuma amfanin ta yaci gaba, watau “Sadaƙa mai Gunana” ko bayan ran mai ita.

## LAFUZZAN DA AKE AMFANI DA SU WURIN BAYAR DA WAKAFI

Waƙafi na da lafuzza bayyanannu ga su kamar haka:

- Na bayar da (abu kaza) a matsayin waƙafi.
- Na tsare shi daga magada na.
- Na bayar da shi fisabililLahi.

Amma lafuzzan kinaya a wurin aiwatar da waƙafi, sune kamar haka:

- Na bayar da sadaka.
- Na haramta wa kaina shi.
- Na bayar da shi har abada.

## SHARUDDAN WAKAFI

Anyi sharaɗi ga wanda zai yi waƙafi cewa, dole sai ya dace da Shari’ah. Watau tilas mai bayar da waƙafi ya kasance kamar haka:

• Ya kasance ya cancanci bayarwa, ba na fashi ba ne, ba kuma ya saya ba ne amma bai karɓa ba domin ya mallake shi tabbatacciyar mallaka ba.

• Ya kasance wanda zai yi waƙafi mai hankali ne. Ba ya halatta waƙafin mahaukaci ko maras wayo da sauran su.

• Ya kasance ya balaga, ba ya halatta waƙafin ƙaramin yaro, ko mai wayo ne ko maras wayo.

• Ya kasance mai lura, waƙafi ba ya halatta ga wanda yake wawa ko gafalalle.

## SHARUDDAN ABUBUWAN DA ZA'A YI WAKAFI DA SU

Domin waƙafi ya kasance, ga sharuɗɗa a kan abubuwan da za'a yi waƙafi da su kamar haka:

• Ya kasance dukiya ce tsayayya, kamar gida ko gona, ko Masallaci, ko waninsu.

• Ya kasance an iyakance abin da aka yi waƙafi da shi.

• Ya kasance abinda aka yi waƙafi da shi an mallake shi lokacin da aka yi waƙafin.

• Ya kasance abinda aka yi waƙafi da shi sananne ne, domin ba'a yin waƙafi da abinda ba'a sani ba.

• Ya kasance abinda za'a yi waƙafi da shi babu haƙƙin wani a ciki.

• Ya kasance abin zai amfanar idan aka yi waƙafi da shi.

• Ya kasance amfanuwar abun waƙafin ta halatta.

# RUFEWA

Allah Ya sa duk abinda aka rubuta a wannan Littafi ya zama alheri gare mu baki ɗaya, kuma Allah Ya gafarta mana duk wani kuskure da aka yi a cikin Littafin, domin duk ɗan Adam ajizi ne. Kuma ina roƙon duk wanda ya karanta wannan Littafi da ya yi aiki da abinda ke cikin sa wanda ya yi muwafaƙa da *Kitab-was-Sunnah*, kuma ya gyara duk abinda bai yi muwafaƙa da su ba; bayan haka ya aiko ma ni ko ya aika ma Kamfanin Ɗab'in Littafin domin a gyara. **Allah Shi Ne Mai Sanin Komai.**

**نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين**